RIJIYA GABA DUBU 3

Lokacin da jarumi Imhal da sadauki Darwaz suka ruguntsume da azababben yaki a tsakiyar filin fadar birnin misra wanda yan kallo sama da mutane miliyan dari suka kewaye, sai filin ya cika da ihu da shewar jama'a, nan fa kowa ya cika da mamakin yadda Imhal ke iya kare hare-haren sadauki Darwaz har yake mai da martani, sai da aka day lokaci mai tsawo ana wannan artabu, daya daga cikin jaruman biyu bai samu nasarar Koda kwarzanar jikin daya ba,Al'amarin da yasa jikin sarki taryan yayi Dan sanyi kenan, kuma ransa ya baci, bai San sanda ya mike tsaye ba daga kan karagar sa ta mulki ya fara yiwa jarumin sa kirari, abinda sarki taryan bai taba yiba kenan a tarihin gasa da ake yi tsawon shekaru, Koda sadauki Darwaz ya ga sarkin sa ya mike tsaye Daga kan karagar sa yana Koda shi,sai ya fusata ainun ya kara zage damtse iya karfin sa ya dinga kaiwa Imhal Sara da suka da dukkan karfin sa,cikin wata irin sabuwar jarumtaka mai tsananin zafin nama ta BAZATO, Nan fa shima Imhal ya dinga yin iya kokarin sa don kare kansa,amma sai ya zamana cewa dakyar yake iya kare hare-haren, kuma baya iya mai da martani, Koda ganin haka sai murna ta kama sarki taryan ya dinga shewa, Ai kuwa sai jama'ar gari suma suka dinga taya shi,ya zamana cewa babu mai yiwa jarumi Imhal jinjina a filin, Duk abinda yake faruwa sarki gurzalu yayi shiru yana guntun murmushi kawai don yasan wanene Imhal, A gaba dayan filin gasar babu wanda hankalin sa ya dugunzuma ainun bisa ganin halin da jarumi Imhal ya shiga sama da Gimbiya Shumaira, domin duk sanda taga an kai masa wani mugun gari sai kaga ta kai da kai kamar ita ake kaiwa, wani lokacin ma har mikewa take yi tsaye zumbur! kamar zata kwalla ihu,ita kuwa Gimbiya lamirat kawai tana kallon fadan ne,ba ta ma San jarumin da take so ba acikin ranta, amma kuma sanda ta tuno da bayanin da mahaifin ta sarki gurzalu ya gaya mata cewar idan Imhal ya samu nasarar lashe wannan gasar JARUMTA sai ya ga bayansu sai ta ji ta tsani Imhal fiye da komai a duniya, domin babu abinda take so sama da sarki gurzalu da mahaifiyarta, ana cikin haka ne sadauki Darwaz ya kara kuntata Imhal har ya matse shi a waje daya ya hana shi matsawa, kuma ya cigaba da kai masa Sara da suka na hauka ba sassauci, ai kuwa sai ya samu nasarar dankara masa Sara a saman kirjin sa,take Imhal ya kwalla ihu ya fadi kasa a lokacin da jini yayi tsartuwa daga kirjin nasa, Koda Darwaz yaga Imhal ya fadi kasa sai ya kai masa suka da takobi a ciki, Cikin zafin nama Imhal ya goce ya doki marainansa da kafa, kawai sai ji akayi Darwaz ya kurma uban ihu ya fadi can gefe daya, a sannan ne Imhal ya mike tsaye dakyar jini na zuba kirjin sa yana yin layi,Cikin sauri ya cire wani yanki dake daure a goshin sa ya daure raunin don ya rage zubar jinin, a sannan ne Darwaz ya mike tsaye zumbur! ya kwarara uban ihu bisa ganin ya samu nasarar yiwa Imhal rauni, A sannan ne fa sarki taryan ya cigaba dakyakyata dariyar mugunta, Koda suka had a idanu da sarki gurzalu sai gurzalu yayi masa murmushin mugunta ba tare da nuna karayar zuciya ba,Al'amarin da yasa jikin sarki taryan yayi Dan sanyi, kuma ya daina kyalkyala wannan dariyar muguntar,A wannan lokacin Imhal ba karamin kokari yayi ba ya tsaya bisa kafafunsa, don jiri ne yake dibarsa sakamakon jinin da ke zuba daga kirjin sa kuma idanunsa suna lumshewa yana gani dishi-dishi,Koda Darwaz ya lura da irin halin da Imhal ke ciki sai ya bushe da dariyar mugunta don yasan cewa yanzu ne zai gama da Imhal farat daya.

zan cigaba

RIJIYA GABA DUBU 3 CIGABA 1

Kawai sai Darwaz ya gyara tsayuwarsa, sannan sannan ya sake zaro wata sharbebiyar adda a bayansa wato ya hada makamai guda biyu a hannun sa yana mai gyara tsayuwarsa gami da

fuskantar Imhal, A sannan ne fa filin gasar ya rude da shewar jama'a, Attajiran da suke yin caca akan gasar suka dinga yiwa junansu kirari, Kaso bakwai cikin kaso goma na 'yana cacar duk sadauki Darwaz suka zaba a matsayin jarumin su,kaso uku ne kacal suka yi kundunbala suka zabi Imhal, tun da ake yin caca a wannan gasar ba a taba zuba kudade masu yawa ba irin na bana,Da yawa Daga cikin attajiran da suka shiga wannan caca idan ba jarumin su ne yaci gasar ba karayar arziki tazo musu kenan.
Lokacin da jaruman biyu suka fuskanci juna, sai filin gasar yayi tsit! aka zuba Ido don ya ga wanda zai yi nasara, saboda ansan cewa wannan gamon da za ayi na karshe ne, Koda Darwaz ya ga shima Imhal cike yake da burin neman sa'a, sai ya budi baki ya karanta wadansu Dalasumai na tsafi guda biyu, kawai sai Imhal yaga wata irin gagarumar iska ta kanannadeshi tasa ya kasa Koda daga hannun sa,ko matsawa daga inda yake, kuma sai Darwaz ya rugo izuwa kansa yana mai daga makamansa sama yana ihu, Abin al'ajabi shine, babu wanda yaga wannan guguwa wacce ta kanannade jarumi Imhal face sarki gurzalu, domin shine kadai yake da karfin ganin sihirin tsafin Darwaz,Imhal yayi iya kokarin sa akan ya kaucewa guguwar ya kasa,Al'amarin da ya dugunzuma hankalin sa ke nan yana ganin mutuwa muraran, Koda sarki gurzalu yaga abin da ke shirin faruwa sai yayi nuni da hannun sa izuwa kan guguwar da ta kanannade Imhal don ya kawar da ita ,amma sai nasa sihirin tsafin ya ki yin tasiri, Take ya tuna cewar ai Yau ya manta bai dauro gurunsa na tsafi ba ya barshi a can cikin wata akwati a dakin da aka sauke shi,nan take bakin ciki ya rufe shi ya sunkuyar da kansa kas yana mai rufe fuskarsa don baya son Darwaz ya samu nasarar kashe Imhal, A dai-dai wannan lokaci ne hankalin Shumaira ya dugunzuma ainun bisa ganin za a hallaka jarumin da taji ta kamu da tsananin sonsa a Yau dinnan kuma farat daya,kawai sai ji tayi hawayen bakin ciki ya zubo mata.Gaba daya attajiran da suka zabi Imhal a matsayin jarumin su suka zuba kudin su na caca akansa sai jikinsu yayi sanyi, suka ayyana cewar asara tazo musu tunda gashi suna gani an durfafoshi da gudu za a sare shi,amma ko motsi ya kasa yi,Koda ya rage bai fi taki uku ba kacal Darwaz ya iso kan Imhal ba sai ya daka tsalle sama da nufin ya sare kan Imhal da makaman dake hannun sa,wato takobi da adda, Kwatsam!ba zato ba tsammani sai Imhal yaji guguwar da ta kanannadeshi ta sake shi ta bace bat!t take ya samu damar sunkuyawa ya kaucewa harin da Darwaz ya kawo masa ,makaman Darwaz din suka sari iska, kafin Darwaz ya juyo da baya tuni Imhal ya soka masa takobi a gadon baya, takobi ta burma gadon baya ta fito ta cikin sa ,Darwaz ya kwarara ihu saboda tsananin zugin sukan da akayi masa ,sannan ya fado kasa yana shure-shuren mutuwa, Ai kuwa sai attajiran da suka zabi Imhal a matsayin jarumin cacar su suka kaure da ihu gami da shewar farin ciki, Gimbiya Shumaira kuwa bata San sanda ta daka tsalle ba sama don murna ta kama kyalkyala dariya, amma tana hada ido da sarki taryan sai taga ya kame, saboda tsananin mamaki da takaici, fuskarsa ta murtuke babu alamar annuri ko kadan, Sarki gurzalu da 'yarsa Gimbiya LAMIRAT kuwa, suma sai farin ciki ya lullube su suka kama yiwa Imhal tafi. Sauran 'yan kallo kuwa kamewa suka yi kamar gumaka saboda tsananin mamaki bisa ganin yadda aka gama dajarumi Darwaz farat!daya, duk da cewar babu kamar sa a karfin damtse da karfin sihirin tsafi a garin,shi kuwa jarumi Imhal yayi matukar mamaki yadda akayi ya tsira daga sharrin wannan guguwar tsafin, Haka ma sarki gurzalu yayi wannan mamaki, kuma hankalin sa ya Tashi, ya fara tunanin cewa lallai akwai wani ma'abocin tsafi da ya taimaki Imhal daga cikin'yankallo,don haka ya zama wajibi yayi bincike don ya gano ko wanene, nan take ya ayyana a ransa cewar yana komawa turakar da aka sauke su zai daura

gurun tsafin sa don yayi binciken.Ana cikin wannan halin ne aka ga jarumi Imhal ya yanke jiki ya fadi kasa,Koda ganin haka sai Gimbiya Shumaira ta yunkura za ta ruga izuwa cikin filin inda Imhal yake, amma sai sarki taryan ya ruko hannun ta yana mai daka mata harara, take ta shiga taitayinta ta sunkui da Kanta kasa cikin alamun kunya.
ZAN CIGABA.
RIJIYA GABA DUBU 3 CIGABA 2
A wannan lokaci ne sarki taryan ya umarci likitansa yaje ya ceci rayuwar Imhal, a guje likita ya isa filin gasar ya kama aikin sa na ceton rayuwar Imhal tare da dinke masa saran da Darwaz yayi masa,nan take aka dauke gawar sadauki Darwaz Daga filin gasar sai sarki taryan ya ba 'yarsa Gimbiya Shumaira izuwa cikin gidan sarautar, Al'amarin da yasa filin gasar ya watse kenan, kowa ya kama gaban sa,shi kuwa sarki gurzalu da Gimbiya LAMIRAT sai suka wuce izuwa masaukin sarki gurzalu, shi kuwa jarumi Imhal bayan likita ya gama dinke raunin da ke kirjin sa yasa masa magani sai aka dauke shi aka kai Shi izuwa cikin wannan daki mai kama da kurkuku aka kulle shi.
Lokacin da sarki gurzalu suka isa cikin masaukinsu suka zauna, sai wata kuyanga ta kawo musu ruwan inibi suka Sha,a lokacin da fuskar sarki ta cika da annuri yana ta farin ciki amma sai yaga gimbiya lamirat tayi shiru tana mai sunkui da Kanta kasa cikin alamun damuwa, Gurzalu ya dubi LAMIRAT yace, Yake 'yata,ina dalilin wannan damuwa taki? Koda jin wannan sai lamirat ta kawo gwauron numfashi ta ajiye sannan ta dube shi cikin alamun tsananin damuwa ta ce,Ya kai Abbana akan wane dalili kake farin ciki alhalin babban makiyin mune ya samu nasara a wannan gasa? sabo dame kake son lallai kayi wannan gasa da jarumi Imhal alhalin na gani da idanunka cewar shi mutum ne mai tsananin sa'a? shin baka tunanin cewa kana neman kayi ganganci ne da rayuwarka akan jarumi Imhal? maimakon kai ceci rayuwar sa kamata yayi kasa a kashe shi,ko a sirrance ne kai bani dama a daren Yau nayi baddakama naje har dakin da aka kulleshi na kashe shi.Kafin lamirat ta gama rufe bakin ta tuni sarki gurzalu ya daka mata tsawa har ta firgita taji hantar cikinta ta kada,ta Dan na da baya kadan Daga kusa dashi, Koda yaga ta firgita sai ya bushe da dariya, sannan ya dubeta cikin nutsuwa da murmushi yace,Haba yake 'yata, shin kin manta da ko ni waye ne? NINE FA MURUCIN KAN DUTSE,WANDA BAN FITO BA SAI DA NA SHIRYA! NINE SA GUDU, MAGANIN KI GUDU! KUMA NINE BAKIN TAKOBI MAI RABA MASOYA! Ina mai tabbatar miki da cewar na gama yin bincike a cikin halwar tsafi na gano cewa idan har ba ta hanyar wannan gasar jarumtaka ba,bazan samu damar hallaka shi ba,duk da cewar na gwada jarumtaka ta da tashi,naga karfin mu yazo daya, ai yanzu zanyi amfani ne da karfin sihiri na,na hallaka shi a yayin da muke yin wannan gasa,ni yanzu Abu daya ne ya shige min duhu, kuma ba komai bane na fuskanci cewar akwai wanda ya taimaki Imhal da sihirin tsafi a Yau lokacin da ake wannan gasa,kuma bansan ko waye ba, amma yanzun nan zan bincike na gane ko waye.Koda gama fadin hakan sai sarki gurzalu ya mike tsaye ya shige cikin kuryar dakin da ya kwana inda akwatinsa ta ke,da Isarsa gaban akwatin wacce ta kasance katuwar gaske mai nauyi, kuma wacce ke datse da katon kwado,sai ya kurma uban ihu, Cikin firgita lamirat da dakarun sa dake can kofar turakar suka rugo izuwa cikin dakin, A dimauce LAMIRAT ta dubeshi tace,Me ya faru ya kai Abbana kai kurma uban ihu haka? maimakon ya bata amsar tambayarta sai ya juyo a fusace ya fuskanci wadannan dakaru nasa masu tsaron dakin yace, Bayan mun  tafi filin gasar JARUMTA waye ya shigo cikin dakin nan? Shugaban Dakarun ya risina yace, Ya shugabana babu wanda ya shigo,

in baka manta ba kai da kanka na kulle dakin da mukulli da zaka fita ,kuma yanzu ma da kai dawo kai ka bude shi da hannun ka... Kafin badakaren ya rufe bakinsa tuni Sarki gurzalu ya sare takobinsa cikin bakin zafin nama ya fille masa kai, sai ga jini yana tsiri izuwa saman dakin ta cikin jijiyoyin wuyan badakaren, sannan kuma sai gangar jikin ta fadi kasa rub da ciki,Faruwar hakan ke da wuya sai ragowar dakarun suka firgita ainun suka dauke gawar dan'uwansu da sauri suka fice da ita,A sannan ne sarki gurzalu ya dubi lamirat a lokacin da idanunsa suka kada suka yi jawur yace,Wani yazo ya sace min gurun tsafina, maza ki tafi neman wannan barawo a cikin garin nan,shine wanda ya taimaki Imhal a filin gasa. Da jin haka sai LAMIRAT ta juya da sauri ta tafi izuwa can bangaren da turakar sarki taryan take domin ta sanar dashi abinda ya faru kuma ta nemi izininsa akan tafiya cikin gari don farautar barawon mahaifinta.
to jama'a zan cigaba idan na huta.
RIJIYA GABA DUBU3 CIGABA 3
Lokacin da sarki taryan ya tafi da Gimbiya Shumaira izuwa cikin turakarsa, bayan Angama wannan gasar JARUMTA, sai ya tunkude ta ta fada kan wata doguwar kujera, ya dubeta cikin fushi har muryarsa na rawa yace,akan me Zaki so jarumin da yake fada da nawa jarumin?sabo dame Zaki nuna soyayyar ki a fili gaban jama'a ki zubar da kimarki da mutuncin gidan nan?Shin kinsan irin makudan kudaden da nayi asara a wannan gasa bisa kudin da na zuba a cacar da mukayi ni da sarki gurzalu? Lokacin da sarki taryan yazo nan a jawabinsa sai gimbiya Shumaira ta sunkui da Kanta kasa cikin biyayya tace,ka gafarceni ya kai Abbana, ka sani cewa a rayuwata ban taba son wani da namiji ba a rayuwata ba face wannan bakon jarumi, kai da kanka kayi mini tayin 'ya'yan sarakai guda ashirin da uku a wannan nahiya amma nace akai kasuwa, idan baka manta ba na gaya maka cewar, bazan yi aure ba face na samu jarumi mai tsananin sa'a da JARUMTA, kaga kuwa lallai babu wanda ya dace dani face wannan bakon jarumi tunda gashi sa'arsa ta bayyana a fili, tunda gashi ya kashe jarumin da babu kamarsa, alhalin a zahiri bai isa ya iya da shi ba.Yayin da sarki taryan ya ji wannan batu sai jikinsa yayi sanyi, kuma hankalin sa ya dugunzuma yayi shiru ya kasa cewa komai, kwatsam! sai ga wani babban hadimansa ya shigo cikin turakar sa,hadimin ya risina ga sarki taryan yace,ya shugabana Gimbiya LAMIRAT 'yar sarki gurzalu tazo yanzu, tace tana son ganinka cikin gaggawa, Koda jin wannan batu sai mamaki ya kama sarki taryan tare da Gimbiya Shumaira suka dubi juna sannan ya dubi hadimin yace, he ka kace ta shigo,nan take hadimin ya fita sai ga gimbiya LAMIRAT ta shigo fuskar ta a murtuke babu annuri, kai da gani kasan cewa tana cikin tashin hankali, LAMIRAT ta risina ga sarki taryan tace,Ranka ya dade barawo ne ya shiga cikin masaukin Abbana ya sace masa wani Abu mai darajar gaske.Koda jin wannan batu sai mamaki ya turnuke sarki taryan da Gimbiya Shumaira, sarki taryan ya dubi lamirat yace, Tun da aka gina gidan sarautar nan tsawon shekaru dari da goma Sha daya ba a taba yin sata ba a cikin sa sai Yau,lallai ko wane ne yayi wannan sata ya cika hatsabibin gaske, domin nasan irin tsaron da yake gidan nan yafi gaban misali, ko sarkin barayin aljanu yana shakkar yazo yayi sata a  nan, wai shin mene ne abinda aka satar muku? lallai zan sa a tsananta bincike har a kamo wannan barawo, kuma ki gayawa mahaifin ki cewar komai kimar abinda aka sace masa zan biya shi.lokacin da gimbiya lamirat taji wannan batu sai ta gyada kai cikin alamun takaici tace,Inda zaka cika gidan sarautar nan taka da darhami, baza ka iya siyan abinda aka sacewa ubana ba,ni yanzu abinda ya kawo ni gareka shine, ka bani izinin shiga cikin gari don farautar wannan barawo, kuma ka bani dakarun ka wadanda za suyi mini rakiya, wadanda suka San

sirrin birnin ka sosai, in yaso kayi naka binciken daga baya, Koda jin wannan batu sai sarki taryan ya sake kamuwa da tsananin mamaki, kuma hankalin sa ya dugunzuma ainun, nan take ya tura aka kirawo masa wani badakare mai suna DARHUS, ya dubeta shi yace, maza ka debi jama'arka mutum dubu uku Ku tafi tare da Gimbiya lamirat izuwa cikin gari, lallai ina son Ku bincika gida-gida,lungu-lungu da duk wani sako da ke cikin garin nan domin Ku gano barawon da yayi wa mahaifin ta sata har cikin masaukin da na bashi, kada Ku dawo gareni face kun kamo wannan barawo, idan bakwa son Ku fuskanci fushi na.nan take DARHUS ya risina yace, Angama, kawai sai ya juya da sauri ya fice daga cikin turakar, Gimbiya lamirat ta bishi da sauri.
A wannan rana dai sai da hankalin gaba daya mutanen birnin misra ya tashi, domin sama da dakaru dubu arba'in DARHUS ya diba bisa jagorancin gimbiya LAMIRAT suka dinga shiga gida-gida,unguwanni da kasuwanni suna dukan mutane suna caje kayayyakin su ana neman abinda aka sacewa sarki gurzalu.
Zan cigaba
RIJIYA GABA DUBU3 CIGABA 4

Duk gidan da aka shiga sai an tarwatsa kayan ciki anyi filla-filla da su kin a duk Inda aka riski bako tasa ta same shi domin anfi tsananta bincike a kansa saboda sai anfara yi masa dukan tsiya anyi laga-laga da shi sannan ma za a fara tuhumarsa, Tun safe aka fara wannan bincike amma har dare ya raba ba a ga abinda ake nema ba,kuma ba a ga wanda ya dauke abin ba,Bisa dole su Gimbiya lamirat suka hakura suka koma gidan sarautar suka sanar da sarki gurzalu da sarki taryan abinda ake ciki, nan fa hankalin sarakunan ya kuma dugunzuma fiye da ko yaushe, musamman ma sarki gurzalu wanda ya tabbatar da cewar duk burinsa na duniya ya rushe idan har ba a ga wannan Abu da aka sace masa ba,nan fa sarki taryan ya sake dimaucewa bisa ganin yadda hankalin sarki gurzalu ya Tashi ainun, don haka sai ya sake baza dakaru izuwa cikin birni da kauye kai har izuwa cikin dazuzzuka ma yace duk inda aka ga wadansu baki a kamo su azo dasu Koda kuwa sun kasance fatake ne masu wucewa,haka kuwa al'amarin ya kasance aka yi ta kamo baki ana kai su kurkuku ana kullewa, har sai da babban kurkukun birnin ya cika fal sannan aka dinga kaiwa sauran kananan gidajen maza da ke wurare da bam.A wannan dare dai sarki gurzalu bai yi bacci ba har gari ya waye bisa tsananin tashin hankalin da yake ciki.
Ba wani abu aka sacewa sarki gurzalu ba face gurunsa na tsafi wanda shine kadai abinda ya dogara da shi akan cewar yana bashi sa'a a gasar jarumtakar da akeyi a birnin misra tsawon shekaru, abinda ya fi razana shi shine, yanzu yaya zai yi da batun shiga wannan gasa,ya sani cewa saura wasa biyar ga jarumi Imhal su hadu a filin gasa su fafata, Koda yake dai yanzu Imhal bashi da lafiya, dole ne yayi jinya ta tsawon Koda kwana bakwai ne,kuma ya San cewa ko babu wannan gurun tsafi a tare dashi ba ya shakkar karo da Imhal domin Idan har bai samu nasarar kashe shi ba sai dai ayi RAGAS indai da zallan karfin damtse da kwarewar yaki za suyi fadan, babban abin tashin hankali shine, barawon da ya sace gurun tsafin sa ba karamin sihirin tsafi ne da shi ba tunda har ya iya shiga har cikin masaukinsa ya sace gurun ba tare da asirin sa ya tonu ba kuma tabbas zai cigaba da taimakon Imhal a cikin wannan gasar jarumtaka da ake yi har ya kai ga nasara.
Abinda ya fadowa sarki gurzalu a rai shine, yana da zabi guda biyu rak! Ko dai ya koma can birnin Kisra ya shiga halwar tsafin sa yayi bincike don ya gano ko waye wannan barawo da

kuma inda yake kafin a cigaba da gasar JARUMTA, ko kuma duk yadda za ayi ya gano barawon kafin gasar tazo kansa,nan fa sarki gurzalu ya rasa hukuncin da ya kamata ya yanke, Babu yadda sarki taryan bai yi ba don ya San abinda aka sacewa sarki gurzalu amma abun ya gagara, domin yaki ya gaya masa,Dama ya dameshi da tambaya sai yace dashi, Abinda aka sace mini yafi komai da kowa daraja a idanu naka wannan duniya, tunda sarki taryan yaji wannan batu sai yayi shiru bai kara yi masa magana ba.kashe gari kuwa tun kafin hasken rana ya fito su Gimbiya lamirat suka sake bazama izuwa cikin gari neman barawon sarki gurzalu. Al'amarin Gimbiya Shumaira kuwa,a wannan rana sai ts rasa sukuni, domin ta kasa zaune ko tsaye, kuma ta kasa yin bacci, ba komai ne ya janyo hakan ba face duk sanda ta runtse idanunta bata ganin komai face jarumi Imhal, nan take taji tunani da begensa sun addabe ta kuma taji bata da sauran kwanciyar hankali idan bata je ta gan shi ba,domin gani take kamar mutuwa zai yi sakamakon wannan Sara da jarumi Darwaz yayi masa a kirji, nan fa Shumaira ts fara tunanin hanyar da zata ni taje ta ga jarumi Imhal a can inda aka tsareshi, Samun wannan dama kuwa ba karamin aiki bane saboda babu wanda yake da ikon zuwa wannan wuri face sarakunan biyu wato sarki taryan da sarki gurzalu domin dokar da aka kafa kenan tun jiya da aka kai Imhal aka tsare, Koda Shumaira taga tunanin yayi mata yawa ta kasa komai sai ta fito daga cikin turakar ta,A wannan lokaci da ko wanka ba tayi ba,kuma tana sanye ne da rigar bacci wacce ke nuna dukkan siffofin jikinta, kawai sai ta kama kai kawo a cikin harabar turakar ta ta inda kuyanginta ke ta kai kawo suna yi mata aiyuka iri-iri, kwatsam! sai ta hango wata kuyanga ta taho za ta gifta ta gabanta,tana kallon fuskar kuyangar sai ta ga ai bakuwa ce domin bata taba ganin fuskarta ba.Al'amarin da yai matukar bata mamaki kenan domin babu yadda za'ayi a kawo bakuwar kuyanga cikin turakarta ba tare da an sanar da ita ba,Har kuyangar ta gifta ta zata wuce sai Shumaira ta Sha gabanta da sauri suka dubi juna,tsawon 'yana dakiku sannan Shumaira tace, Wacece ke kuma yaushe aka kawoki nan,muhallina ba tare da sani na ba?Koda jin wannan batu sai kuyangar tayi murmushi cikin alamun takama da yarda da kai tace,Ni ba kuyangar ki bace hanya ce ta biyo dani ta nan,bani hanya na wuce abina idan ba so kike ranki ya baci ba, Koda jin wannan batu sai ran Gimbiya Shumaira ya baci bisa ganin cewa tana matsayin'yar sarki amma kuyanga tayi mata rashin kunya, kawai sai ta daga hannu da nufin ta sharawa kuyangar mari,amma sai taji hannun nata ya makale a sama ta kasa sarrafa shi,kuma taji an matse hannun nata,wani irin mugun zugi da radadi na shigarta bata San sanda ta fara ihu ba,Abinda ya daure mata kai shine,duk ihun da take yi babu mai jinya,asalima babu wanda yaga abinda ke faruwa, nan take tsoro ya kama Gimbiya Shumaira ta fara tunanin cewa,lallai wannan kuyanga da ke gabanta ba mutum bace aljanna ce.
zan cigaba.

RIJIYA GABA DUBU3 CIGABA 5

Koda ta ayyana hakan a cikin zuciyar ta sai ta dubi bakuwar kuyangar cikin tsananin dauriya tace,Ki gafarceni banyi dai-dai ba,kafin ta gama rufe bakinta sai taji an saki hannun ta kuma ta daina jin zafin komai, kawai sai ta sake duban kuyangar tace,"Ya ya akayi kika sami damar shigowa gidan nan ,alhalin babu wani aljani da ya taba shigowa tun farkon gina shi? " sanda bakuwar kuyangar taji wannan tambaya sai tayi murmushi tace,Ni ba aljana bace, mutum ce ni kamar ke,idan har kina so kisan ko ni Wacece ki kaini cikin turakar ki mu zauna muyi wata magana, bayan hakan ne za kisan ko ni wace ce kuma zan taimaka miki na kaiki har inda aka tsare bakon jarumi ki ganshi ba tare da kin fuskanci wata matsala ba,Koda jin wannan batu sai

murna ta kama Shumaira nan take ta kama hannun kuyangar ta ka ta izuwa can cikin turakar ta,da shigarsu cikin kuryar dakin kuyangar ta zauna tana mai yin hamma alamar cewa tana jin yunwa da bacci, har Shumaira ta budi baki za tayi magana sai ta dakatar da ita da hannu tace,Kafin muyi maganar komai sai naci na koshi, maza kisa a kawo min abin kalaci,Koda jin haka sai gimbiya Shumaira ta kwalawa wata kuyangarta kira tace da ita,taje ta kawo mata abin kalaci,Koda jin wannan umarni sai mamaki ya kama kuyangar mai suna SALIFAT, Salifat ta sunkui da kai kasa tace,"ya shugabata me za kiyi da abincin kalaci yanzu alhalin dazu na kawo miki kika ce bakya bukatar?" Shumaira ta dakawa Salifat tsawa tace,"Ina ruwan ki,yanzu nake bukatar cin abincin, maza kije ki dauko mini kafin raina ya baci".Cikin hanzari kuyangar ta juya da sauri ta je ta dauko abincin bisa faranti a cikin manyan kwanuka guda biyu na dinare, kuyanga Salifat tazo ta ajiye farantin a gaban bakuwar kuyangar amma kuma ba ta ganta ba,bata ma San cewa akwai wani mutum a cikin dakin ba face Gimbiya kadai,Koda kuyangar ta ji kamshin abinci ya doki hancinta sai ta fado kasa Daga kan kujera ta bude kwanukan abincin ta duma hannu a ciki ta kama ci kamar wacce ta shekara da yunwa, kafin a jima ta cinye kusan rabin abincin dake cikin kwanukan biyu wanda a ka'ida mutum shida ne ke iya cinye shi,tana gamawa ta dauki tambulan din ruwan ta shanye shi tas ya zama ko digo daya bata rage ba sannan tayi wata katuwar gyatsa,kai da gani kasan cewa bata saba cin abinci mai daraja ba irin wannan, A sannan ne bakuwar kuyanga ta mike tsaye ta koma kan kujerar ta zauna sannan ta fuskanci Gimbiya Shumaira ta dubeta cikin nutsuwa tace,"sunana MUZAIRA, kuma ni 'yar uwar matar sarkin Kisra ce na da,wanda sarkin yanzu ya kashe ya hau karagar mulkinsa. "Koda jin wanne batu sai Shumaira ta mike tsaye zumbur! cikin alamun tsoro da mamaki, kuma jikinta ya kama tsuma tana mai nuna MUZAIRA da dan yatsa bakinta na rawa tana so tace wani abu amma sai ta kasa,Koda ganin haka sai MUZAIRA tayi murmushi tace," kwantar da hankalin ki ya ke Gimbiya Shumaira, ban zo nan dan cutar da ke ba,sai domin na taimake ki kamar yadda nayi alkawari,kuma kema ki taimake ni,wannan bakon jarumi da kika kamu da son sa wato jarumi Imhal da ne a waje na,domin MAHAIFIYARSA yayata ce,uwar daya uba daya,kuma na biyo shi ne izuwa birnin misra domin na ceci rayuwar sa a cikin GASAR JARUMTAKAR da ake yi,Tabbas a dazu sanda ya fafata da sadauki Darwaz, in ba don na kawo masa dauki ba da tuni Darwaz ya hallaka shi da karfin sihiri, inda kin lura za kiga cewar jarumi Imhal ya tsaya cak a waje daya sanda Darwaz ya rugo da gudu izuwa kansa a wannan lokaci wata guguwar sihiri ya jefo masa ta kanannadeshi ya kasa Koda motsa hannayensa,nice na kawar masa da guguwar a lokacin da saura kiris Darwaz ya gama dashi.

Yanzu zan gaya miki wani babban sirri wanda ba ki San shi ba,kuma labarin zai girgiza kwakwalwarki, da farko dai nice barauniyar da ake ta nema a cikin garin nan da kewayensa wacce tayi wa sarki gurzalu sata, kuma ba wani abu na sace masa ba face wani GURU na TSAFI indai yana tare da wannan grun tsafi babu wani mahaluki da ya isa ya samu nasara a kansa,ko ya iya cutar dashi, yanzu gashi Gurun ya dawo hannu na, koda MUZAIRA tazo nan a zancen ta sai ta yaye rigar da ke jikinta, take Shumaira tayi arba da gurun tsafin zagaye a kugun MUZAIRA, MUZAIRA ta saki rigar ta rufe gurun sannan ta cigaba da cewa, Albarkacin wannan guru ne na samu damar shigowa gidan nan ba tare da kowa ya ganni ba,kuma abinda sarki gurzalu bai sani ba shine, tun kafin su shigo cikin garin nan na sace gurun a wani lokaci da suka ya da zango a cikin daji ya fita daga cikin tantinsa yaje yayi wanka a wani rafi.

zan cigaba

RIJIYA GABA DUBU3 CIGABA 6

Dama ina biye dasu tun daga can birnin kisra a cikin siffar wata tsuntsuwa basu sani ba,A lokacin na shiga cikin tantin nasa,kuma nayi sa'a na iske akwatinsa a bude, ya manta bai kulle ta ba bayan ya dauki mayafin da zai tsane ruwan jikinsa bayan yayi wankan, Bai taba mancewa da kulle wannan akwati ba sai a wannan lokaci, don haka bayan na sace gurun tsafin sai na datse kwadon akwatin ,shi kuwa dan mabudin kwadon akwatin dama ko da yaushe yana jikin mazagin wandonsa.

Lokacin da ya dawo cikin tantin nasa ya iske akwatinsa a rufe bai iya tunawa cewa a bude ya barta ba,Bayan na mallaki gurun tsafin ne jiya na shiga har cikin turakarsa na bude akwatin da karfin sihiri, kuma na barta a bude domin nasa shi zargi cewa a nan ne aka sace Gurun.

Yanzu zan baki labarin abinda yasa na sace wannan Guru.

Nan take Zumaira ta bawa labarin duk yanda akayi aka yanka mahaifiyar Imhal aka kaita daji aka yar ana zaton ta mutu har tsoho imzanu ya ganta ya ceci rayuwar ta kuma ta cigaba da rayuwa a cikin hauka har izuwa sanda ta haifi jarumi Imhal, a karshe ta mutu ta barshi a hannun tsoho imzanu ya cigaba da rainonsa har ya girma, kawo izuwa sanda sarki Gurzalu ya tura a kashe tsoho imzanu a kamo Imhal har izuwa cikin gari inda suka fada cikin gidan ta ta taimake su.

Koda MUZAIRA tazo dai-dai nan a labarin ta,sai taga hawaye na zuba a idanun Shumaira sakamakon tsananin tausayi da ta ji bisa jin tarihin rayuwar Imhal da yadda aka yiwa iyayensa kisan gillah, Nan take Shumaira taji ta tsani sarki gurzalu don jin mugun zaluncinsa, kuma ta kudurce a ranta cewar lallai sai ta raba alakar dake tsakaninsa da mahaifinta sarki taryan, Koda Zumaira taga Shumaira na kuka,sai itama zuciyar ta ta karaya ta fashe da kukan aka rasa wanda zai rarrashi wani har izuwa tsawon 'yan dakiku sai daga can Shumaira ta nutsu ta daina kuka ta dago kai ta dubeta tace,Yanzu wane irin taimako kike so nayi miki? Koda jin wannan tambaya sai Zumaira ta nutsu tace,Ba wani taimako nake so kiyi mini ba face ki ajiye duk abinda na fada miki sirri a cikin zuciyar ki har izuwa ranar gasar Imhal ta karshe, wato ranar da zai fafata da sarki gurzalu domin idan kika gayawa Imhal cewar sarki gurzalu ne ya kashe iyayensa ya hau karagar mulkin a yanzu duk shirin mu ya watse baza mu iya daukar fansa ba akan sarki gurzalu, domin Imhal zai hau kace ne yace yanzu-yanzu zai dauki fansa,kinga kuwa ba zai iya ba,tunda sarkin yawa yafi sarkin karfi,karfi.

Inda dai ace nasan sirrin yadda ake amfani da wannan gurun sihirin ne na sarki gurzalu da nayi amfani dashi wajen hallaka shi, abinda zan iya yi yanzu kawai shine, nacigaba da boye wannan gurun tsafi a waje na har izuwa ranar da zasu fafata shi da Imhal ya zamana cewa ta kowane hali bai bar hannuna ba,domin indai gurzalu baya tare da gurun tsafin, bazai iya samun nasara ba akan Imhal,sirri daya na sani na amfani da wannan gurun, wato sirrin bata,duk wanda yake tare da wannan gurun da wanda ke tare dashi ba a ganinsu, kuma ba a jin muryarsu Koda kuwa za suyi ta tsandara ihu, su kwana suna yi,yanzu sai ki tashi kiyi mini jagora izuwa inda aka tsare Imhal domin na ganshi ko ma samu 'yar nutsuwa, amma baza muyi masa magana ba ,don ko munyi ma bazai ji ba ,ba tare da gardamar komai ba Shumaira ta mike tsaye ta kama Zumaira ta ka ta suka fice daga cikin gidan sarautar suna ta ratsawa ta cikin lunguna da sakuna, suna tafe suna hira abin su,kuma gashi duk inda suka ratsa akwai dakaru a tsaitsaye suna rangadi amma babu mai ikon ganinsu ko jin muryarsu, duk inda suka je kuma suka iske kofa a rufe basa bukatar su bude sai dai kaga sun ratsa ta cikin karfen kofar sun wuce, tamkar yadda danshi ke

tsatstsafowa daga cikin kasa,Albarkacin wannan gurun tsafin dake daure a kugun MUZAIRA hakan ke faruwa, A haka dai suka iso kofar dakin da aka sa jarumi Imhal a ciki. da yake kofar dakin anyi tane da sandunan karfe sai suka ganshi kwance a kasan dakin ko shimfida babu yana ta faman shara baccin wuya, Koda suka ga halin da yake ciki ,kuma suka ga katon raunin dake kan kirjin sa sai suka fashe da kuka, Tabbas duk wanda ya dubi Imhal a wannan yanayin da yake dole ne ya tausaya masa domin numfashinsa ma yana fita ne da sauri-sauri kamar ba zai rayu ba,sai da suka dade a tsugune a wajen suna kallon sa sannan MUZAIRA ta zura Kanta ta cikin sandunan kofar da hannun ta guda ta shafa kan Imhal, a lokacin da hawayen idanun ta ya zubo akan kumatunsa, shafa kan nasa ke da wuya ya farka daga bacci, Koda ya ji danshi a kumatunsa sai ya shafo shi ya duba, Koda ya fahimci cewar ba ruwa bane,hawaye ne,sai ya mike tsaye zumbur! ya kama waige-waige amma bai ga kowa ba,A lokacin ne Shumaira tayi sauri ta kama hannun MUZAIRA ta janye ta suka bar wajen.
zan cigaba.
RIJIYA GABA DUBU3 CIGABA 7
Nan take Imhal yaji a jikin sa cewar lallai wata ce tazo wajen sa har tayi kuka hawayen ta ya zuba akan kumatunsa, Amma abin tambayar shine,Shin Wacece wannan mai zubar da hawaye saboda tausayinsa? Amsar da ya kasa baiwa kansa kenan, shi dai a sanin sa bashi da kowa a wannan duniya wacce zata zubar da hawayen ta saboda tausayinsa, nan dai jarumi Imhal ya fada kogin tunani inda ya tuno da abokin sa MARIGAYI ZAUWADU kuma ya tuno da wasiyyar da ya bar masa sanda ya bashi wata sarka yace dashi, lallai komai dadewa yaje unguwar sharkas a cikin birnin kisra ya nemi masoyiyarsa SUHAILA ya bata wannan sarka, kuma ya bata labarin rayuwar su a cikin kurkuku har izuwa lokacin da ajali ya riske shi,Koda yazo nan a tunaninsa sai hawaye ya zubo masa yaji yana fatan ya rayu ya sake kubuta Daga sharrin sarki gurzalu domin yaje ya sauke wannan alkawari da ya daukarwa abokinsa Zauwadu.
Wannan shine abinda ya faru tsakanin Gimbiya Shumaira da Zumaira kanwar mahaifiyar jarumi Imhal wacce itama take da burin daukar fansa akan sarki gurzalu.
Al'amarin sarki gurzalu kuwa, lokacin da su Gimbiya LAMIRAT suka sake shafe wuni guda suna neman barawon sa a cikin birni da kauye suka dawo babu nasara, sai sarki gurzalu ya zama kamar mahaukaci ya dinga buge-buge da iface-iface, da kyar!LAMIRAT ta shawo kansa ya dawo hayyacinsa, sannan ta dube shi tace,Ya kai Abbana yanzu mene ne dalilin da ya hana ka tashi na garzaya izuwa can birnin kisra domin kar shiga dakin halwar tsafin ka ka binciko wanda ya sace maka gurun nan?Koda jin wannan tambaya sai sarki gurzalu yayi aniyar zuciya yace, Abinda yasa naki komawa birnin kisra shine tunda nake zuwa wannan gasa tsawon shekaru talatin baya ban taba komawa gida ba a lokacin da aka gasar ba,idan na koma mutane za su iya cewa na tsorata ne da abokin gwamina ko kuma na karaya na koma gida don nayi sabon shiri, kinga kenan yanzu duk zabi biyun da nake dasu akan matakin da ya kamata na dauka duk sun rushe, muna ji muna gani kenan makiyanmu za su iya samun nasara akan mu.
Koda jin haka sai lamirat ta gyada kai tace, Haba ya kai Abbana, hanyar kashe makahon kare yawa gareta, ina da wata dabarar, cikin mamaki da zumudi sarki gurzalu ya dubi lamirat yace, Ya ke'Yata wace irin dabara kike tunani? lamirat ta numfasa tace,Ni ina ganin cewa ka saka sarki taryan ya kirawo maka gaba daya bokayen kasar nan su dukufa akan binciken gano barawon ka,indai bokayen kasar nan suka hada karfi da karfe, lallai zasu iya gano barawon ka a cikin kwanaki kadan kafin Imhal ya sami lafiyar da zai iya cigaba da wannan gasa har

haduwarka dashi tazo, Koda jin wannan shawara sai farin ciki ya lullube sarki gurzalu yace, ina alfahari dake 'yata tabbas kinyi dogon tunani mai kyau, to amma fa dole ne muyi la'akari da irin raunin dake jikin Imhal mu kiyasce iya tsawon lokacin da muke ganin zai warke, idan kuma yazo dai-dai da sanda Bokayen za su samu nasarar gano barawon shikenan bamu da sauran damuwa,amma idan har Imhal ya samu lafiya kafin su gano barawon akwai matsala babban,Lamirat tace, kada ka damu ya Abbana, duk zan kula da hakan, kuma a Yau dinnan za a gama komai, Koda gama fadin haka sai Gimbiya lamirat ta mike tsaye ta fice daga cikin dakin,bata zame ko ina ba sai turakar sarki taryan, bayan anyi mata iso ta shiga inda yake sai ta risina ta gaishe shi sannan tace, ya shugabana, Abbana ne yace nazo na nemi alfarmar zuwa ganin jarumi Imhal, Koda jin haka sai sarki taryan ya girgiza kai yace,Ai bazan iya baki wannan dama ba domin yana daga cikin dokar wannan gasa ba a barin abokin gasa yaje ya gana da dan'uwansa,idan har kika je kika gana da Imhal kamar sarki gurzalu ne yaje tunda kin kasance 'yarsa,Lamirat tace,na yarda ka hadani da amintattun Hadimanka su rakani gareshi, idan ana zargin ko zanje na cutar dashi ne,,Koda jin haka sai sarki taryan yayi shiru yana tunani, daga can kuma sai yayi aniyar zuciya yace,shikenan na amince, Take lamirat tayi godiya, ba tare da bata lokaci ba aka hadata da wadansu amintattun Hadimai su hudu gami da dakaru dari suka tafi izuwa dakin da aka kulle jarumi Imhal.
Da isarsu suka iske jarumi Imhal a kishingide a jikin bango yana con abinci dakyar kamar zai yi amai ko Riga babu a jikinsa sakamakon katon raunin da ke kirjin sa.
Tun daga nesa jarumi Imhal ya hango Gimbiya lamirat tare da dakaru sai ya kura mata idanu yana mai yi mata murmushi.
Zan cigaba
RIJIYA GABA DUBU3 CIGABA 8
Ita kuwa Koda taga yana yi mata murmushi sai ta murtuke fuskarta tamkar taga bakin kumurci(Bakin maciji mai masifa da mugunta) kuma sai ta dinga satar kallon raunin da ke kan kirjinsa, tana nazari da tunanin adadin kwanakin da take ganin cewar ciwon zai iya warkewa har ya iya cigaba da yin wannan gasa.
Lokacin da Gimbiya lamirat suka iso daf da kofar dakin sai suka tsaya cak! Akayi tsit! ana kallon-kallo tsakaninta da jarumi Imhal, kawai sai Imhal ya dubeta fuskarsa cike da annuri yace,"Mene ne ya kawoki wajena,ko kuwa kinzo ne ki karasani saboda kina tsaron karona da mahaifinki? "
Koda jin wannan tambaya sai murmushi ya subucewa Gimbiya lamirat bata sani ba,ta dubeshi cikin gadara tace, "Ai matsoraci baya kusantar abokin gaba,nazo ne domin naga lafiyar abokin gaba, domin idan ka mutu yanzu sai nafi kowa bakin ciki, saboda bani da burin da yafi na sare kanka da hannun nan nawa".
Koda jin wannan batu sai mamaki ya kama jarumi Imhal yace," Wai shin menene dalilin da yasa keda mahaifinki kuka tsananta kiyayya a kaina,alhalin babu wani mugun sabani da ya taba shiga tsakanina da Ku? shin ta yaya Zaki samu damar sare kaina da hannunki alhalin bakya cikin wannan gasa ta KAMBUN JARUMTA? Koda ma kina cikin wannan gasa ni bazan iya kashe ki da hannu na ba,domin a cikin fadin duniya kaf a yanzu babu abinda nake kauna sama dake".
Koda jin wannan batu sai lamirat da gaba daya dakaru da hadiman dake bayan ta suka cika da tsananin mamaki, lamirat ta fusata ainun, ta dakawa Imhal tsawa tace,"Kai talaka, makaskanci!

ka sani cewa wutsiyar rakumi tayi nesa da kasa,kuma RUWA da WUTA basa haduwa, batun soyayya a tsakani na dakai babu har abada sai kiyayya! Nayi maka alkawarin cewar wannan karon baka isa ka kubuce ba daga sharrin mu face munga karshenka!!"
Koda jin wannan batu sai jarumi Imhal ya bushe da dariya, lokaci guda kuma ya hade fuska yace,"Ni kuwa nayi miki alkawari sai kin nemi gafarata da murya mai taushi, kuma kin rokeni na So kind......!!!"
Kafin jarumi Imhal ya rufe bakinsa tuni lamirat ta tofa masa yawu a fuska tace,"Da dai na SO ka har na furta maka kalmar SO gwara na rasa rayuwata, kuma ka saurari ranar da za kayi gasa ta uku, nice abokiyar gwaminka ".
Tana gama fadin haka sai tayi sauri ta juya cikin fushi zuciyar ta na tafasa tamkar zata kone, cikin hanzari hadimai da Dakaru suka bita a baya.
Shi kuwa jarumi Imhal sai yasa hannun sa ya lakuto yawun da lamirat ta tofa masa a fuska ya shanye shi yana murmushi yace, " Ba a soyayya da karya... kuma ba a kiyayya da karya, na kamu da tsananin sonki Gimbiya lamirat, kuma bazan daina sonki ba Koda Zaki zamo sanadin ajalina!
Yana gama fadin haka sai ya koma ya kwanta a kasa, kansa yana kallon Rufin dakin yana murmushi gami da mamakin yadda akayi radadin SO ya sa shi ya bayyana soyayyarsa a fili a Yau ba wadda ta tsane shi kamar yadda ta tsani ajalinta, kuma ya cigaba da wasu-wasi a cikin zuciyarsa akan cewar; "Wai shin da gaske ne Lamirat ce abokiyar gwaminsa ta uku a cikin wannan Gasar Jarumtaka?"
Abinda baiwa sani ba shine, shi kansa sarki gurzalun baiwa San cewa Gimbiya lamirat ta shiga cikin wannan gasa ba,don tun kafin su iso birnin ta aiko da wasika mai dauke da hatiminta da sa hannunta ba sarki taryan tace lallai a sata a matsayin jarumar da zata fafata a karo na uku da bakon jarumin da za su zo dashi ".
Koda sarki taryan yaga wannan wasika sai ya cika da dimbin mamaki, amma da yaga hatimi da sa hannun ta sai yasa aka rubuta sunanta a cikin jaruman gasar.
Wani iko na Allh kuma sai ya manta ya tambayi sarki gurzalu dalilin da yasa ya bar Gimbiya lamirat ta shiga cikin wannan gasa.
Bayan lamirat ta baro wajen Imhal sai ta koma izuwa turakar sarki gurzalu ta gaya masa cewa," Dole ne Bokayen da za su kira suyi musu wannan bincike su kammala a cikin kwanakin da basu wuce bakwai ba,saboda na tabbatar da cewar kafin Imhal ya warke har yaji karfin da zai iya fitowa filin gasa sai ankai kwana bakwai ".
Sanda sarki gurzalu yaji wannan batu sai fuskar sa ta fadada da murmushi, yace," Ai faduwa tazo dai-dai da zama, domin tuni na gana da shugaban bokayen kasar nan a Yau bayan na rabu da ke, kuma har ya tabbatar mini da cewar nan da cikar kwanaki bakwai dai-dai za su gano mini Barawon,tabbas aikin ki yayi kyau.
zan cigaba
RIJIYA GABA DUBU3 CIGABA 9
Da jin haka sai farin ciki ya lullube Gimbiya lamirat tayi godiya kuma sai fuskarta ta sauya yanayi izuwa matukar damuwa ta sunkui da Kanta kasa tana mai yin shiru,Al'amarin da ya tayar da hankalin sarki gurzalu kenan ya dubeta shima cikin damuwa yace, "Ya ke 'yata me ya faru,kuma naga fuskarki ta sauya yanayi daga farin ciki zuwa kishiyarsa?" Sanda ta ji wannan tambaya sai ta dago kai a lokacin da idanun ta suka kada suka yi jawur kamar hawaye zai zubo

mata tace,"Ya kai Abbana a iya sanina a cikin tarayya ta dakai ban taba yi maka karya ba kuma ban taba yi maka laifi ba,ko ba haka bane?"
Cikin mamaki sarki gurzalu ya gyada kai yace,"Tabbas tun daga kuruciyarki kawo izuwa girmanki baki taba yi min wadannan abubuwan biyu ba".
Lamirat tace,wannan karon nayi maka wani laifi tun kafin mu baro gida, kayi hakuri bazan iya gaya maka wannan laifi ba sai bayan an kammala wannan gasa ta khango JARUMTA, amma ina rokonka da ka yafe min wannan laifi tun kafin ka San shi"
Koda Gimbiya lamirat tazo nan a zancen ta sai sarki gurzalu ya sake kamuwa da tsananin mamaki, yayi shiru yana tunani da nazari har izuwa tsawon dakiku, daga can sai ya dubeta cikin murmushi yace, "Na yafe miki wannan laifi'Yar Lele,kuma ko bayan na San laifin na rantse da girman abin bautarmu bazan yi fushi da ke ba"
Koda jin haka sai farin ciki ya kama lamirat ta rungume sarki tana mai yi masa godiya, nan dai lamirat tayiwa sarki gurzalu sallama ta tafi izuwa masaukin ta,wato dakin Gimbiya Shumaira.
Tana shiga dakin sai ta hango Shumaira zaune tana sarrafa hannayen ta alamar cewar tana yin magana ne da wani.
Amma da lamirat ta karaso cikin falon sai taga Ashe babu kowa a cikin falon, Shumaira ce kadai a zaune.
Al'amarin da yayi matukar bata mamaki kenan, ta dubi Shumaira tace,Shin akwai wani aljani da yake zuwa wajen ki kuyi hira?
Cikin mamaki Shumaira ta dubi lamirat tace,Ai babu wani aljani da ya isa ya shigo cikin gidan sarautar nan domin iyaye da kakanni sun gama shirya gidan da tsari na musamman.
LAMIRAT tace,"Wannan gaskiya ne,domin mahaifina ya tabbatar min da haka, amma yanzu da na tunkaro wannan falon naki naga kina sarrafa hannayenki alamar cewa kina yin magana ne da wani "
Koda jin haka sai Shumaira tayi murmushi tace,A'a babu wanda nake hira da shi ,kawai dai ina tunani ne gami da zancen zuci ,
Cikin sanyin jiki Lamirat ta zauna a gefen Shumaira suka yi shiru tsawon'yan dakiku kadan.
Duk wannan abu dake faruwa MUZAIRA na zaune a gefe daya tana hararar lamirat, kuma jikinta na tsuma, ji take kamar ta mike zumbur! ta je ta shake Gimbiya lamirat har sai ta kasheta saboda kiyayya.
Ita kuwa lamirat gashi dai tana fuskantar kujerar da MUZAIRA take zaune a kai amma ba ta iya ganinka,Shumaira kadai take iya gani a cikin falon.
Daga can sai lamirat ta katse shirun da suke ciki ta dubi Shumaira tace,Ya ke kawata ina son zan baki wata shawara guda daya, shawarar kuwa ita ce,Kada ki so saurayin da ba shine ya fara nuna soyayyarsa ba a gareki, domin watakila kiyi SON MASO WANI.
Koda jin wannan batu sai mamaki ya kama Gimbiya Shumaira tace, Ke kuwa mene ne dalilin da yasa kika fada mini wannan magana alhalin ban taba gaya miki cewar ina son wani saurayi ba?
Koda jin haka sai lamirat tayi murmushi tace, Tun da dai nayi miki hannun ji mai sanda baki gane ba bari na fito fili nayi miki baro-baro watakila za ki fi fuskantar inda nasa gaba.
Idan za ki iya tunawa, a ranar da aka fara gasar kambun JARUMTA tsakanin jarumi Imhal da sadauki Darwaz sai da kowa ya gane cewar kin kamu dason jarumi Imhal sakamakon nuna matukar tashin hankali bisa ganin zai hallaka da kuma yadda kika nuna farin ciki lokacin da ya samu nasara, to ina mai tabbatar miki da cewa jarumi Imhal yana da tsananin so da bege a

cikin zuciyar sa,kuma har ya fito fili ya bayyana mata sirrin zuciyar sa,sai dai kashe! Anyi rashin sa'a,domin wacce yake so din ta tsane shi kamar yadda ta tsani mutuwarta, bisa wannan dalili ne na gaya miki cewa ki taka a hankali, kada kiyi SON MASO WANI wanda hausawa suke cewa KOSHIN WAHALA.
Na baki wannan shawara ne a matsayinki na tsohuwar kawata da muke tare tun kuruciya,sannan idan kunne ya ji jiki ya tsira,shawara kuma ta rage ga mai shiga RIJIYA.
Koda gama fadin hakan sai Gimbiya lamirat ta mike tsaye ta shige cikin dakin bacci ta kwanta domin ta huce gajiyar da tasha a ranar SAKAMAKON yawon da suka Sha na farautar barawon mahaifin ta.
Ita kuwa Gimbiya Shumaira sai taji zuciyarta ta buga da karfi, tunani da wasu-wasi suka cika mata ranta bisa kokarin gano ko Wacece budurwar da jarumi Imhal ya kamu da tsananin sonta haka?
Koda MUZAIRA taga hankalin Shumaira ya dugunzuma ainun sai ta mike tsam! Daga kan kujerar da take zaune ta koma wajen ta ta dafa kafadunta ta dubeta tace,"Kwantar da hankalin ki ranki ya dade,a matsayina na uwa a gun jarumi Imhal in dai ina numfashi a doron kasa sai na siyo miki soyayyars Imhal,domin kece kika dace dashi fiye da kowace budurwa a wannan duniya, domin soyayyarki a gareshi, soyayya ce ta gaskiya, wacce babu algus! a cikin ta".
Koda jin wannan batu sai hankalin Shumaira ya kwanta ta rungume MUZAIRA tana mai yi mata godiya gami da fatan samun nasara akan makiyansu.
Zan cigaba,
RIJIYA GABA DUBU3 CIGABA 10
Kwana Uku cur!da Faruwar wannan al'amari ne sarki gurzalu na tsalle-tsalle gami da yin wasa da takobi a wani babban fili dake cikin harabar gidan sarki taryan don baiwa kansa horon yaki, sai ga 'yarsa Gimbiya LAMIRAT ta durfafoshi sanye cikin shigar yaki kuma rike da takobi, Al'amarin da ya bashi mamaki kenan, ya tsaya cak! ga barin baiwa kansa horon yaki har ta iso daf dashi sannan ya dubeta yace,"Yake 'yata,ina dalilin fitowarki a wannan lokaci, kuma a cikin shigar yaki? "
Koda jin wannan tambaya sai lamirat tayi murmushi tace,"Ya kai Abbana kayi sani cewa Yau kusan shekaru uku kenan rabon da mu wasa jini ni da kai,don haka ina son mu dan fafata domin na gani ko na samu cigaba a koyon yaki na fiye da abinda ka koya mini a baya tunda a kullum a cikin neman Karin ilimi nake."
Koda jin haka sai sarki gurzalu yayi murmushi yace, "Wannan ba laifi".
Nan take ya gyara tsayuwarsa, ita ma sai ta tsaya a nesa kadan dashi ta gyara tsayuwarta suka fuskanci juna,Daga can kuma sai suka fara zagaya juna,
Kamar hadin baki sai suka ka da baya a lokaci guda sukayi taku uku kacal, sannan suka rugo da gudu izuwa kan juna suka kacame da masifaffen yaki, ya zamana cewa suna kaiwa juna SARA DA SUKA cikin azababben zafin nama,juriya da bajinta, suna neman hallaka juna da dukkan karfinsu tamkar sun kasance tsofaffin abokan gaba,
Tunda suka fara wannan gumurzu sarki gurzalu ya cika da tsananin mamaki, domin a saninsa Sam gimbiya lamirat bata da zafin nama irin na yanzu, kuma kwarewarta a yaki ba ta kai hakan ba.
Abu dai kamar a mafarki sai gashi karfinsu ma yazo daya,an rasa wanda zai iya cutar da dayan. Sai da suka shafe rabin sa'a suna fafatawa a cikin wannan hali, Al'amarin da ya fusata sarki

gurzalu kenan, ya sauya salon yakin ya hada da kai mata bugu da naushi hannu da kafa.
Kawai sai yaga ita ma ta koma irin salon da ya koma kuma ya kasa cutar da ita,da kyar da sidin goshi ya shammaceta ya daka wawan tsalle sama ya doketa da kafa a fuska,
Tana faduwa kasa a lokacin da lebenta ya tsage, jini ya dan zubo, sai ita ma ta kwarfi kafafunsa yai sama ya rikito kasa,amma sai ya duro bisa kan tafin hannunsa guda cikin bajinta ya doki kasa da tafin hannun nasa yai sama ya dawo kasa bisa kafafunsa.
A dai-dai wannan lokaci ne suka ji ana yi musu tafi, suna waigowa baya suka ga Ashe sarki taryan ne tare da 'yarsa Gimbiya Shumaira suka durfafo inda suke, cikin hanzari lamirat ta mike tsaye tana mai goge dan jinin da ke kan lebenta da tafin hannunta.
Sarki taryan ya dubi Gimbiya lamirat yace,"Hakika wannan 'ya ta gaji ubanta a jarumtaka, lallai yanzu ne nasan cewa kin cancanci ki shiga.,...."
Kafin ya karasa fadin abinda ke bakinsa sai Gimbiya lamirat ta tari numfashinsa don kada ya tona ma ta asiri tace,"Ai barewa ba ta gudu danta yayi rarrafe.
Ya shugabana me yasa kazo ka katse mana wannan horon yaki da muke yi?"
Koda jin wannan tambaya sai sarki taryan yayi ajiyar zuciya yace, "Ai wani gagarumin abin mamaki ne ya faru yanzu shine nace lallai sai nazo na sanar da Ku, yanzun nan na kaiwa jarumi Imhal ziyara a dakin da aka tsareshi, ina zuwa sai na iske likitana yana cire zaren da aka dinke wannan rauni na kirjin sa,ina mai tabbatar muku da cewa raunin ya hade ya warke sumul tamkar ma bai taba yin sa ba".
Koda jin wannan labari sai sarki gurzalu da Gimbiya LAMIRAT suka kallo junansu cikin fargaba da tsananin mamaki.
Sarki taryan yaci gaba da cewa," A halin yanzu dai jarumi Imhal yace a shirye yake ya cigaba da wannan gasa gobe, don haka na sanar da duk Alkalan gasar tuni ma an cigaba da shirye-shirye."
Koda sarki taryan yazo nan a zancen sa sai sarki gurzalu yayi ajiyar dogon numfashi yace,"Wace irin magana kake yi haka kamar Almara? Ya za ayi ace mutum ya samu irin wannan babban rauni, kuma ace ya warke a cikin kwanaki uku kacal? "
Sarki taryan yace ai kada kayi mamaki da hakan, domin akwai mutane masu baiwar saurin warkewa daga ciwo, idan baka manta ba ai har a cikin RIJIYA GABA DUBU ta kurkukun DARUL MAUT aka sa jarumi Imhal ana yi masa azaba har tsawon kwanaki, amma aka fito dashi a cikin kwanaki kadan duk raunin dake jikinsa suka warke, kuma ya samu lafiyar jikinsa.
Koda jin wannan batu sai sarki gurzalu da gimbiya lamirat suka kalli juna cikin alamun damuwa da takaici, sannan lamirat ta dubi sarki taryan tace,"Wanene wannan jarumin da zai fafata da Imhal gobe? "
Sarki taryan ya jinjina kai yace "Wani bakin jarumi ne shima daga birnin Askandariyya,nima ban taba ganinsa ba,sai gobe a filin gasar za muga ko wane ne".
Koda gama fadin haka sai sarki taryan ya kama hannun gimbiya Shumaira suka juya suka nufi inda suka fito.
Suna cikin tafiya ne Gimbiya Shumaira ta juyo ta kalli sarki gurzalu da Gimbiya lamirat ta ga ko kadan babu annuri akan fuskokinsu, tamkar an aiko musu da sakon mutuwa, kawai sai tayi musu wani irin guntun murmushi wanda suka kasa fahimtar ko na mene ne tsakanin na mugunta ko na alhini.
Shi kuwa sarki taryan sai ya dubi Shumaira yace, Hakika yanzu na fara yarda da zargin da nake

yi akan sarki gurzalu, domin ban ga dalilin da yasa suka tsananta kiyayya ba akan jarumi Imhal,bisa binciken da nayi ma tun farkon haduwar Imhal da sarki gurzalu laifin da yayi masa bai kamata ayi masa hukuncin dauri a kurkukun Darul Maut ba balle har a sanyashi a cikin RIJIYA GABA DUBU a azabtar dashi na tsawon kwanaki ba,tabbas an zalunceshi, ni kuwa a rayuwata bana son zaluntar mutumin da yake kasa dani,musamman wanda ya kasance talaka na".
Koda Gimbiya Shumaira taji wannan batu daga bakin mahaifinta sai farin ciki ya lullube ta domin ta fuskanci cewa hakanta zai cimma ruwa a kokarin da take yi na raba alakar da ke tsananin sa da sarki gurzalu, tunda gashi shi da kansa ma ya fara gano irin zaluncin sarki gurzalu.
Zan cigaba
RIJIYA GABA DUBU3 CIGABA 11
A daren wannan rana aka cigaba da shela a cikin birane da kauyukan kasar misra ana sanar da cewa, "Lallai gobe da safe za a cigaba da gasar kambun JARUMTA.
Ai kuwa tun a cikin daren 'Yan kallo suka dinga tururuwa a cikin filin gasar don kada su rasa inda za su zauna suyi kallo.
yayin da gari ya waye kuwa sai ya zamana cewa duk inda mutum ya duba a filin gasar babu masakar tsinke, ko ina kawunan bil'adama ne rututu.
Kai! har kan katangar filin gasar mutane ne a zazzaune maza da mata,a tsakiyar filin ne kawai aka bar hanyar da za a wuce don shigowar sarakai gami da jaruman gasa da alkalai.
Sai da aka shafe kusan rabin sa'a ana jira sannan aka ji tambura na tashi gami da bushin Algaita alamar cewa sarakai za su shigo filin gasa,Nan fa filin gasar ya rude da shewar jama'a suka kamu da tsananin murna don sanin cewa yanzun nan za a fara gasar.
Ai kuwa sai ga sarki taryan, sarki gurzalu, da 'ya'yayensu mata tare da sauran manyan sarakuna na nahiyar sun shigo cikin filin gasar dakaru na biye da su a gaba da baya, gefe da gefe, ana cigaba da buga tambura, har sai da suka isa inda mazauninsu yake suka zauna.
Zaman su ke da wuya sai mai gabatar da gasar ya mike ya fara jawabi yana mai yiwa manyan baki barka da zuwa, sannan ya sanar da cewar jarumin da ya fara wannan gasa,wato jarumi Imhal ya warke daga raunin da ya samu a cikin kwanaki uku kacal,kuma da shi za ayi wannan gasa ta Yau kamar yadda dokar gasar ta tanadar cewa,duk jarumin da ya samu nasarar lashe gasar ba zai yi fashin wasa ba face baya numfashi a doron kasa,kuma komai yawan raunikan da ke jikinsa indai zai iya warkewa sai an jira shi ya warke har izuwa tsawon mako biyu, idan ya wuce mako biyu ne bai warke ba an cire shi daga cikin jaruman gasar,
Lokacin da jama'a suka ji cewar jarumi Imhal ya warke daga ciwon sa a cikin kwanaki uku kacal sai kowa ya kamu da tsananin mamaki aka shiga yi masa jinjina da kirari tun kafin ma ya fito filin gasar,nan fa filin ya rude da shewa gami da hayaniyar mutane har sai da aka buga gangar fara gasa sannan aka yi tsit! tamkar mutuwa ta fado filin gasar.
A sannan ne mai gabatarwa ya kirawo sunan bakon jarumin da yazo daga birnin Askandariyya wai shi ZAMBARU IBINI KULSAS.
Kawai sai aka ga wani bajimin katon mutum mai tsawon kamu ashirin da bakwai ya fito daga cikin dakin jaruman gasa wanda ya kasance mai kauri da fadin kirji, inda za a yanke kafarsa guda a dorawa mutum dakon ta a kansa,ji zai yi kamar an Dora masa cinyar katuwar giwa.
Koda jama'a suka yi arba da wannan narkeken kato mai kirar mutanen farko, sai suka firgice

suka dimauce ainun, domin gani suka yi kamar zai baje filin gasar gaba daya ya mutsittsike kowa da komai da ke filin.
Nan fa jama'a suka kama mikewa tsaye domin su ruga da gudu izuwa wajen filin gasar,sai da dakaru suka hau daka musu tsawa sannan kowa ya nutsu ya koma mazauninsa.
Duk sanda Zambaru yayi tafiya taku daya sai a ji birnin gaba daya yayi girgiza kamar kasa za ta tsage komai da ke samanta ya rufta cikin ta, Kai hatta sarki Gurzalu da ya kasance jarumin da ke rike da KAMBUN JARUMTAKA sai da ya firgita bisa ganin Zambaru, Ya Sha jinin jikin sa,ya ayyana cewar lallai babu tabbacin shi kansa zai iya hallaka wannan basamuden kato Koda kuwa da karfin sihirin tsafi ne.
Bayan Zambaru ya iso tsakiyar filin gasar sai ya tsaya ya daga kansa sama yayi wata irin kururuwa mai tsananin kara da firgitarwa wacce ta cika cikin birnin misra da duk kauyukan da ke kewayensa da amsa kuwwa, kuma ta firgita mutane da dabbobi har ma da aljanun dake kawayen wajen.
Al'amarin da ya janyo hargitsewar birnin kenan, mutane suka dinga guje-guje da iface-iface, matan dake dauke da tsohon juna biyu kuwa ba shiri suka kama yin nakuda ta ba zato suka dinga haife abinda ke cikin duba tare da lokacin haihuwar yayi ba,Har sai da Zambaru ya tsuke bakinsa sannan komai ya lafa, mutane suka dawo cikin hayyacinsu.
A wannan lokaci ne mai gabatarwa ya kirawo jarumi Imhal, kawai sai aka ga jarumi Imhal ya fito da gudu daga cikin dakin jaruman gasa rike da takobi da garkuwa cikin shigar yaki ba tare da shakkar komai ba.
Koda ganinsa sai filin gasar ya rude da shewa aka kama yi masa jinjina da kirari, mawaka na yi masa lakabi da SABON JARUMI MAI ABIN AL'AJABI,
Koda Zambaru ya hango jarumi Imhal ya nufo cikin filin gasar a guje rike da wata takobi sai ya zura hannun sa izuwa bayan sa ya fiddo wata lafceciyar takobi wadda inda za a ajiye ta a kasa karti ashirin majiya karfi basa su iya dagata sama ba.
Maimakon jarumi Imhal ya tsaya a sake buga tambarin fara gumurzu, kawai sai ya cigaba da gudu ya tunkaro inda jarumi Zambaru yake tsaye.
Shi kuwa Zambaru sai ya fara wulwula takobinsa a sama yana jiran isowar Imhal.
Yayin da ya rage saura bai fi taku shida ba kacal Imhal ya iso inda Zambaru yake sai ya daka wawan tsalle sama kamar an cilloshi daga baka sai gashi ya iso dai-dai wuyan Zambaru.
Ai kuwa sai ya dankara masa Sara a wuya, take takobin ta makale a jikin wuyan Zambaru tamkar a jikin bishiya mai kauri ta nutse.
Imhal ya finciko takobinsa da hannayensa biyu da dukkan karfinsa amma sai ya kasa Ciro takobin.
Kafin ya sake yin wani yunkuri tuni Zambaru ya mako shi da hannun sa na hagu wanda baya rike da makami, take Imhal ya fado kasa ba shiri ya duro akan kafarsa ta hagu,ai kuwa sai kafar tasa ta karye ya kurma uban ihu sakamakon tsananin zafi da zogin da ya ji ya sulale kasa a matukar galabaice ya kasa mikewa tsaye.
Koda ganin abinda ya faru sai Zambaru ya bushe da mahaukaciyar dariya ta mugunta, sannan yasa hannun sa na hagun ya zare takobin Imhal wacce ta makale a wuyan sa, jini yayi tsartuwa daga jikin wuyan nasa,amma ko a jikinsa.
Kawai sai yayi jifa da takobin ya nufi jarumi Imhal wanda ke zaune a kasa, yana mai daga lafceciyar takobinsa.

Gaba daya 'Yan kallon da ke cikin filin gasar sai suka dafe kai suka fara ihu da kururuwa domin sun San cewa lallai Imhal ya zama gawa tasa ta kare.
Su kuwa attajiran da suka zabi Zambaru a matsayin jarumin gasar su suka sa kudin su na caca a kansa sai suka fara yin tsalle da murna suna kida da rawa don sun San cewar kakarsu ta yanke saka, sun gama zamowa manyan attajirai.
Wadan da suka zabi jarumi Imhal kuwa a matsayin jarumin gasar su sai suka fara kuka suka kamu da tsananin bakin ciki sabo da sun San cewa lallai karayar arziki ta zo musu!!!
YAYA KARSHEN WANNAN GASA ZA TA KASANCE TSAKANIN JARUMI ZAMBARU DA JARUMI IMHAL? TA YAYA JARUMI IMHAL ZAI TILASTAWA GIMBIYA LAMIRAT TA KAMU DA SONSA? SHIN IMHAL ZAI RASA RAYUWARSA NE A CIKIN WANNAN GASA TA KAMBUN JARUMTA KO KUWA ZAI LASHE GASAR NE HAR TA CIKA BURIKAN DA KE GABANSA?INA LABARIN TSOHO IMZANU KUMA A CIKIN WANE HALI YAKE YANZU A CAN BIRNIN KISRA?
Mu hadu a RIJIYA GABA DUBU 4 don jin cigaban wannan kasaitaccen labarin.